Nuwamba 2014 // Muharram 1436

# fim

Fitowa ta 179

Jagorar Mujallun Hausa

N500

## Ishaq da Mandawari sun surfa wa juna zagi a Indiya!

## Mahmud Nagudu
Ina ya shiga ne?



## Yadda na zama farfesa sau biyu
– Abdalla

An tsare Sima a gidan yari

Lere ya zama shugaban gidan rediyo

Gwamnati ta hana sayar da Hausa-Indiya

•

An maida auren Fati KK

•

Cewar Fati Baffa: Ba zan auri mijin Dawayya ba



# UMMI EL-ABDUL
# 'BAN YIN BAKIN CIKI'

# Ban son in yi mulki sai dai malanta har abada

## - Farfesa Abdalla Uba Adamu

● Kuma ya ce batun finafinan Hausa-Indiya sata ce ta saci sata

*Daga* **IRO MAMMAN**



ARANAKUN 17 da 18 ga Satumba, 2014 aka shirya gagarumin biki na ƙasa da ƙasa don karramawa tare da nuna farin ciki da ƙarin girman da shahararren malamin jami'a kuma manazarci, Farfesa Abdalla Uba Adamu, ya samu a fagen ilimi, wato da aka ba shi muƙamin farfesa a karo na biyu. Ya zama *Professor of Media and Cultural Communication* bayan da ma can ya na kan dokin *Professor of Science Education*. Ba a saba ganin haka ba a Nijeriya baki ɗayan ta. An yi taron a Jami'ar Bayero, Kano, inda a nan ya ke koyarwa.

Farfesa Abdalla ya bada gagarumar gudunmawa ga masana'antar finafinan Hausa ta hanyar ayyukan nazari da ya yi, inda ya sa har aka san finafinan Hausa a sassan duniya ta hanyar Intanet. Hakan ya janyo masana daga ƙasashe da dama zuwa nan ƙasar domin su yi nazarin harkar. Bayan haka, ƙusa ne a fagen nazarin rubutun ƙirƙira na Hausa, inda a nan ɗin ma ya bada gudunmawa mai yawa.

Kada mu manta, Farfesa Abdalla ne ya ƙirƙiro haruffan nan na Hausa masu lanƙwasa a komfutar zamani, wato 'ƙ' da 'ɗ' da 'ɓ', masu sunan *Dr Abdalla Uba Adamu* da kuma *Rabiat Muhammad* (wato *fonts*) waɗanda ake amfani da su wajen rubutun Hausa a komfuta.

Dalilin wannan zango na malanta da ya cimmawa a rayuwar sa ya sa na buƙace shi da mu tattauna kan ayyukan sa a fagen nazari, tare da jin ra'ayoyin sa kan inda ya fito da inda ya ke a yanzu da kuma inda ya dosa. Kuma mun yi sa'a, shehin malamin ya amince, ya amsa tambayoyin baki ɗayan su.

Wannan tattaunawar ta ƙara mana haske ba kurum kan shi kan sa Malam Abdalla ba, a'a, har ma halin da adabin hausa ya ke ciki a yanzu, musamman ɓangaren nazari da kuma finafinai.

Allah shi gafarta Malam, shekara biyu da ta wuce (2012), Jami'ar Bayero ta ba ka mu□amin Farfesa a karo na biyu, wato *Professor of Media and Cultural Communication* a kan Farfesan ka na farko, *Professor of Science Eduation* wanda ka samu a 1997. Ya ka ji a lokacin da ka kai wannan mataki?

Tabbas godiya ta tabbata ga Allah Maɗaukakin Sarki da Ya ba ni wannan damar shiga kundin tarihi a matsayin Musulmi, ɗan Kano, ɗan Arewa na



• Farfesoshi da sauran mahalarta taron babbar laccar Jami'ar Bayero (*Inaugural Lecture*) ta 15 da Abdalla ya gabatar

farko da ya samu muƙamin Farfesa guda biyu a fannoni daban-daban da ba su da alaƙa da juna.

Babban farin ciki na shi ne abu guda ɗaya: buɗe wa masu tahowa hanya. Samun na biyun ya wanke duk wani wanda ake ganin 'haye' ne a wani



• Farfesa Abdalla ya na gabatar da babbar laccar Jami'ar Bayero (*Inaugural Lecture*) ta 15

fagen nazarin da ba shi ne ahalin sa ba. Wannan ita ce babbar nasarar da na samu – yanzu na buɗe ƙofa: duk wanda zai iya bayar da gudunmawa a kowanne fanni na ilimi zai iya yi, ya kai ƙololi, ba tare da jin tsoron gorin da za a yi masa ba, kamar yadda na sha gori kafin a kai inda aka zo yanzu.

Shin da ma hakan ta na faruwa a BUK ko ma Nijeriya ne ko kuwa a kan ka aka fara?

Ba kasafai hakan kan faru ba, ba ma a BUK ko Najeriya ba, ko a duniya ma waɗanda ke da wannan muƙamin ba su da yawa. Akasari mutane in sun samu na farko ma ya ishe su—saboda kafin a je nan ɗin ma sai an kai ruwa rana! Kalilan ne ke canza akalar su, su bazama cikin sabon fage, har ma su kai ga nan ma su zama Farfesoshi. Ni dai sa'a kawai na ci Allah Ya ba ni damar haɗa biyun a lokaci guda.

Kwanan baya ka gabatar da babbar laccar Jami'ar Bayero (*Inaugural Lecture*) a sabon fagen ka na nazari, mai taken *Imperialism from Below: Media Contra-flows and the Emergence of Metrosexual Hausa Visual Culture*. Ko za ka faɗa wa masu karatu bayanan da maƙalar ta ƙunsa a taƙaice?

Wannan babbar laccar ita ce ta biyu da na gabatar a BUK. Na gabatar da ta farko a ranar Asabar, 24 Afrilu, 2004 – shekara wajen shida bayan na zama Farfesan ilimin horon dabarun koyar da kimiyya a 1997. Dalilin jinkirin kuwa shi ne saboda layi ake yi – sai na gaba da ni sun gabatar kafin ni in gabatar; jiran su yi ne ya kai har sai da aka je zuwa 2004.

Wannan ta biyun shekaru biyu kawai na yi ina jira, domin na samu wannan farfesan na biyu a 2012, kuma na gabatar da maƙalar a ranar Laraba, 9 ga Yuli, 2014.

Ga taƙaitccen bayanin maƙalar. Tari da yawa ana ganin laifin finafinan Hollywood (na Amurka) a matsayin masu danne fasahar ƙasashe masu tasowa – ta yadda kowa so ya ke ya kwaikwaye su. Kwatsam, sai Indiya su ka fara yin fim, su ka bazu a duniya. Kafin ka ce kwabo sun zama abin kwaikwayo a wurare da dama a duniya kamar Turkiyya, Giris, Masar, Senegal, Indonesiya, Zanzibar da Ghana. A ko'ina, gani ake finafinan Indiya sun danne na ƙasar da su ka samu kafuwa. Wannan tabbas haka ne a ƙasar Hausa, ta yadda 'yan fim na yanzu su ka rungumi finafinan Indiya a matsayin alƙiblar fasahar su—ko a wanko wani fim kai-tsaye, kuma har alfahari ake yi da yin hakan, ko a yanko wani sashe na fim ɗin a liƙa shi a fim ɗin Hausan, ko



Mataimakin Shugabannin Jami'ar Bayero, Farfesa Abubakar A. Rasheed, ya na taya Farfesa Abdalla murnar kammala lacca

kuma a bi salon bada labarin na Indiya, wanda kan tsagwaron soyayya ne. Wannan danne fasaha ne, domin kamar yadda wani ɗan fim ya ruwaito da bakin sa a wannan mujallar taku shekarun baya, shi dai ba shi da basirar da zai iya yin fim ɗin da zai birge jama'a, saboda haka ya gwammace ya sato na Indiya, kuma ya ce ba zai daina yin haka ba. Wannan juyin wainar shi ake kira *contra-flow*. To ashe ana zaton wuta a maƙera—watau Hollywood—sai ga ta a masaƙa, watau Indiya.

Sannu a hankali finafinan Indiyan su ka fara canzawa, su ka zaƙe su ka fi ma na Amurkan Amerikanci ta hanyar nuna tsiraici da fitar da surar jikin mutum, ko mace ko namiji. 'Yan fim na Indiya kamar su Vinod Khanna, Varun Dhawan, Saif Ali Khan da kuma Hrithik Roshan sun shahara wajen ƙwalisa da kuma nuna ƙwanji, ƙirji da jikkunan su a fim. Wannan ɗabi'ar ta nuna 'mazanci' shi ake kira *Metrosexual*, watau birnanci.

To sai yanzu mu ma an hau salon irin wannan a finafinan Hausa ta yadda za ka ga maza na sa ɗamammun kaya da nuna tsiraicin ƙirjin su—saboda Indiyawa na yi bayan kuma ko a Amurkan ma ba a yi. Kuma tunda 'yan fim na Hausa dole ne su kwafi abin da duk Indiyawa su ke yi, sai birnancin Indiyawa, watau *metrosexuality*, ya zama sabuwar alƙiblar 'yan fim. Watau ka ga tabbacin ana zaton wuta a maƙera kenan, wanda kuma shi ne tabbacin *contra-flow*—watau koma bayan ruwa: maimakon ya ci gaba, sai ya biyo hanya ya dawo baya.

Sannan su kan su finafinan Hausan sun zama wata wutar a waɗansu ƙasashen ta yadda duk inda dandazon Hausawa ya ke, to kwaikwayon fim ɗin Hausa su ke yi. Haka kuma finafinan *Nollywood*, watau na 'yan kudancin Nijeriya, su ma sun zama wata wutar ta yadda suka mamaye Afrikiyya ta Gabas a ƙasashe kamar Uganda, Kenya, Tanzaniya, Malawi, da sauran su. To maƙala ta ta yi magana ne a kan wannan juya-juyar. An saka ta sukutum a wannan rariyar: https://buk.academia.edu/abdalla.

An fi sanin ka a matsayin manazarcin al'adu da adabi, musamman a ɓangaren finafinai da waƙoƙi da littattafan Hausa. To amma kuma asali kai malami ne a sashen nazarin horon koyar da Ilimin kimiyyar halittu (*Science Education*) ne, inda a nan ne ma ka za fara zama Farfesa a 1997. Yanzu ga shi ka na cin tudu biyu a waɗannan sassan biyu. Me ya sa ka raba hankalin ka biyu?

Karatun da na yi tun farko a jami'a shi ne *Biology/Education*, watau horar da malaman da za su koyar da ilimin halittu. Na fara aiki a Jami'ar Bayero a 1980, kuma zuwa 1997 na zama cikakken Farfesa a wannan fannin. A lokacin ina da shekaru 41 a duniya (tun da an haife ni a 1956). A hange na, idan har Allah Ya ara min rai na kai lokacin ritaya, to ina da saura shekaru 24 kenan in yi ritaya a shekaru 65 a lokacin, ko da ya ke yanzu ya zama shekaru 70 ga wanda ya zama Farfesa kafin ya kai waɗansu shekarun.

To magana ta gaskiya, ga ni na ke ba zan iya tsayawa a waje ɗaya har tsawon shekaru 24 ba. Wannan shi ya sa na ce bari in bi wani layin da ni da kai na na ke sha'awa, kuma in shige shi ba da tunanin wai zan ƙure a cikin sa ba. Shi ya sa na karkata akalar nazari na daga 1999 zuwa ilimin sadarwa – watau duk abin da ya jiɓanci isar da saƙo ta ƙirƙirarriyar hanya, wanda aka fi sani da *Mass Communications*. Na fara yada zango ne a hurumin marubuta, daga nan kuma har mu ka zo inda mu ke yanzu.

A wane lokaci ne ka fara sha'awar nau'o'in adabi?

Za a iya cewa tun daga 1996, lokacin da na fara ƙirƙiro da rukunayen haruffan Hausa masu lanƙwasa, kamar ƙ, ɓ, ɗ da yayyen su a manhajar kwamfuta, ta yin amfani da wata manhaja mai suna *Fontographer*. Na yi haka ne kuwa saboda ganin yadda sha'awar karatun littattafan hikaya na Hausa ta bazama tsakanin matasan Hausawa maza da mata. Matsalar da masu sarrafa rubutun a kwamfuta ke fuskanta ita ce rashin waɗannan haruffan. Gudunmawa ta ita ce a samar da su saboda karatun Hausa ya inganta. Alhamdu lillah, an cimma wannan burin, kuma ma yanzu akwai waɗansu da su ma su ka bayar da tasu gudunmawar wajen gyara waɗanda na ƙirƙiro, kuma su ka daɗa ƙirƙirar waɗansu. Haka kam ci-gaba ne mai daɗin gani, ta yadda Hausawa ke amfani da basirar su wajen ciyar da adabi gaba.

Shin shigar ka ɓangaren al'adu da adabi bai jawo maka matsala tsakanin ka da wasu malaman ba waɗanda su ke ganin kamar ka na barin gonar ka, ka na shiga tasu?



Mahalarta taron gabatar da babbar laccar BUK ta 15

Tabbas na samu, to amma wannan ba baƙon abu ba ne a fagen nazari. Ba ma a wancan lokacin ba, har ma a yanzu da mu ke magana da kai a wannan shekarar, ina fuskantar ƙalubale daga waɗansu da ke ganin bai kamata in shigo fagen su ba. Amma duk abin rashin fahimtar abin da na ke yi ne.

Bari in fara da 'yan ahalin adabin Hausa. Ba buri na ne in yi fice a nazarin adabi ba. Shigowa ta ta ta'allaƙa ne a kan dangantakar hanyoyin zamani da sarrafa adabi, kai-tsaye. Amma da na shigo sai waɗansu su ka dinga ganin na yi shisshigi. Na yi ta ƙoƙarin nuna masu cewa ba ruwa na da gundarin adabi—tarihin sa, nau'in sa, surar sa, sarrafa shi, da sauran su—domin ban san waɗannan ba. Da ƙyar na samu dai aka rabu da ni, da aka ga cewa a duk nazari na ko ambaton ayyukan su ba na yi, domin ba nan ne alƙibla ta ba. Amma kuma manazarta na duniya kamar su Brian Larkin (United States) da Graham Furniss (England), nan da nan su ka jawo ni a jiki.

Bayan na fara shigowa tsangayar horon sadarwa, watau *Mass Communications*, a BUK, inda na fara koyarwa na wucin-gadi, watau *part-time*, a 2005 (a 2012 ne na koma din-din-din) nan ma ban tsira ba, domin akwai masu gunagunin ai ba ahali na ba ne.Nan ma na nuna masu cewa ni fa akwai abin da na sa a gaba, kuma in mutum ya na ganin ban yi daidai ba, to ya ƙalubalanci wani rubutu nawa, ya nuna min kuskure na, sai in ƙaru; amma ba a yi ta gurnanin don me ma zan shigo ba. Nan ma a hankali aka rabu da ni. A wannan fagen ne ma manazartan duniya su ka fi jawo ni jiki, ta yadda sai da na fita ƙasashen wajen fiye da sau 25, kuma na gabatar da maƙaloli fiye da 35 a wurare daban-daban. Kai, har koyarwa na yi a Poland na wata uku. Ka ga nan a gida ana gori da gurnanin ba gyara ba dalili, amma kuma a waje ana biɗar mutum ya zo a ƙaru da juna.

Amma duk wa□annan abubuwan ba su dame ni ba, domin da ma haka rayuwar jama'a ta gada – wani zai yi maraba da kai, wani kuma ba zai yi ba. Amma yawan jama'ar da su ka yi murnar shigowa ta duk fannonin biyu – adabi da kuma ilimin sadarwa – ya fi ninkin-baninkin waɗanda su ka koka a kan shigowa ta. A yanzu dai an karɓe ni a duk ɓangarorin, domin ganin cewa ilimi ake yi wa, ba son kai ba. Kuma duk wanda zai bayar da gudunmawa ya zo, domin a ciyar da ilimi da mutanen mu gaba.

A nan ya zama dole in jaddada godiya ta ga Mataimakin Shugaban Jami'ar Bayero, watau *Vice-Chancellor*, Farfesa Abubakar Adamu Rasheed. Shi ne ya ke da hangen nesan tunanin a samar da matakin Farfesa har sau biyu in har mutum ya taka rawar gani a fannin na biyun.

Kuma tun Farfesa Abubakar Rasheed ya na Editan jaridar *New Nigerian* ya ke bibiyar gudunmowar da na ke bayar wa a fagen adabi, saboda haka ya san ayyuka na, da kuma gwagwarmayar da na sha a wajen jama'a. Da ya bar New Nigerian ya dawo BUK a hankali ya zama Muƙaddashin Mataimakin Shugaban Jami'a, watau Deputy-Vice Chancellor. Nan ma ya ga yadda na dinga tafiye-tafiya zuwa ƙasashen duniya domin halartar tarurruka—domin sai na nemi izini, kuma shi ne mai bayar da izinin mafi yawan lokuta—ba tare da na ce jami'a ta ba ni ko sisin kwabo ba.

Da ya hau kujerar Vice-Chancellor ya ga na gabatar da maƙalu da yawa a fagen adabi ta kowannen fanni, kuma har ma finafinan ilimintarwa na yi (*documentary*), sai ya nuna mana hasken cewa in na nemi wani Farfesan a wannan fannin, tabbas jami'a ba za ta ƙi ba. Nan take shugaban soron tsangayar Horon Ilimin Sadarwa, watau *Mass Communication*, Dr. Balarabe Maikaba, ya yi min gurbi a tsarin kasafin kuɗin soron, sannan ya kira taron soron tsangayar inda aka yarda da cewa a gabatar da ayyuka na a matsayin mai neman zama Farfesa a wannan soron. Wannan ba ƙaramin hangen nesa ba ne domin, kada ka manta, ni malami ne a wurin na wucin-gadi. Aka yarda da wannan, sai aka tura wa Tsangayar, watau *Faculty of Social and Management Sciences*, ƙarƙashin jagorancin Farfesa Tanko Adamu, daga bisani su kuma su ka tura wa jami'a cewa sun gamsu. Daga nan kuma aka aika da takardun zuwa ƙasashen Turai domin aunawa. Bayan watanni sakamako ya dawo na cewa na cancanta in zama Farfesa a wannan sabon fannin. Ta haka jami'a ta yarda aka ɗora ni a sabuwar kujerar.



• Al'ummar unguwar Daneji sun ba Farfesa kyautar karramawa

Ba don akwai hangen nesan waɗannan mutanen guda ukun ba, da hakan ba ta faru ba. Wannan shi ne shugabanci, inda ba a ƙyashin ci-gaban jama'a.

**Ko akwai lokacin da jami'a ta nuna maka cewa abin da ka ke yi (wato tsallakawa zuwa wata Tsangayar) ya saɓa wa al'adar malanta a jami'a?**

In ma akwai, to zan ce wani lokaci ne ɗaya kacal da na nemi a ba ni tallafi in halarci wani taro a kan sarrafa tatsuniyoyi a Ingila. Kwamitin da ke da alhakin yin haka ya hana a ba ni tallafin da dalilin cewa ba fage na ba ne! Abin mamakin shi ne a lokacin da na nemi wannan tallafin, ina Jami'ar Warsaw da ke ƙasar Poland ina koyarwa – kuma ɗaya daga cikin abin da na ke koyarwa shi ne sarrafa tatsuniyoyin duniya! Kuma na tafi wannan aikin ne da izinin Jami'ar Bayero!

Amma bayan wannan, kusan duk lokacin da na nemi izini in yi wata



• Taron karrama Faefsa Abdalla a Jami'ar Bayero

tafiya zuwa wani taro a kowane fanni, ana ba ni, musamman dai ganin yadda tallafin tafiyen-tafiyen da na ke yi ba daga Jami'ar Bayero ba ne; duk waɗanda ke gayyata ta su ne ke ɗaukar nauyin tafiye-tafiyen. In Jami'ar Bayero ta ga dama za ta iya hana ni tafiyar da cewa ai ba fanni na ba ne. To amma haka ba ta faru ba, sai dai wancan lokacin kaɗai da na gaya maka.

Kuma na yi ire-iren waɗannan tafiye-tafiye fiye da sau 30. A cikin shekaru goma, daga 2004 zuwa 2014, na gabatar da maƙaloli a Germany (har sau takwas), Nijar (sau biyar), Amurka (sau uku), Ingila (sau uku), UAE (sau biyu), Switzerland (sau biyu), Senegal (sau biyu), Ghana (sau biyu), Ethiopia (sau biyu), Poland (sau biyu), da kuma sau ɗaya a Morocco, Egypt, France, South Africa, Turkey da Cameroon. Sannan na koyar da ɗalibai a University of Florida, Gainsville, da ke United States; University of Cologne da ke Germany, da kuma University of Warsaw da ke Poland, wanda wannan na ƙarshen Tarayyar Turai, watau European Union, su su ka ɗauki nauyin tafiya ta. Yanzu haka ina jiran naɗin in duba wani ɗalibi a University of Beyreuth, Germany. Ina kuma taimaka wa wata ɗaliba a University of Leipzig, Germany.

**An ce an sha ba ka muƙamai na siyasa a gwamnati amma ka na ƙin karɓa, bayan kuwa wasu ma har kamun ƙafa su ke yi domin a ba su. Me ya sa ka ke da irin wannan ra'ayin?**

Na farko, ba a taɓa ba ni wani muƙamin siyasa a kowacce gwamnati ba, a Kano ko a Tarayya. Ba na yin siyasa, ba ni da ra'ayin ta, ba na mu'amala da 'yan siyasa. Kai, hatta rijistar zaɓe ma ba zan yi ba—duk wanda aka zaɓa zan bi shugabancin sa ba tare da adawa ba in dai jama'a ne su ka zaɓar mana shi.

Na ke jin sanin cewa ko da an taya min ba zan karɓa ba ne ya sa mutane ke ganin ko an taɓa taya min ɗin; ko kuma su na ganin kamata ya yi a ba ni ne? Amma nazarin ilimi daban, riƙe muƙami a siyasance daban. Sau dubun dubu gara in tsaya a hurumi na na manazarci! Saboda haka na dai yi ayyuka a kwamitocci a jiha sau ɗaya da kuma Tararraya da dama, amma ban taɓa wani riƙe wani muƙami na siyasa ba, kuma ba na sha'awa ko da nan gaba.

Sannan kuma ganin ma yadda ake tafiyar da siyasar ya sa ba ma zan yi sha'awar karɓar duk wani muƙamin da za a ba ni ba. Kai, hatta kwamitocin ma da aka saka ni na a lokacin waɗansu gwamnatocin, ƙin yarda in shiga na yi—ga dai suna na a cikin kwamiti, amma na ƙi zuwa.

Wataƙila abin da dai mutane ke ta dangantawa da ni dai shi ne na ƙi yarda in shiga takarar neman Mataimakin Shugaban Jami'a, watau Vice-Chancellor, a jami'o'i har uku, watau Bayero University, National Open University, da kuma Kano University of Science and Technology, Wudil. A kowacce daga cikin waɗannan jami'o'in, an nemi in tsaya takara, amma na ƙi. Dalili kuwa shi ne ba na sha'awar mulki ko kaɗan, kuma ba ma zan iya ba, ya fi ƙarfi na. Bincike da yaɗa ilimi da koyarwa shi ne sutura ta, shi ne rayuwa ta, kuma shi ne rufin asiri na. Duk wani muƙamin shugabanci zai yi karo ne da wannan, wanda kuma ba zan so hakan ba.

Sannan kuma na tabbata akwai abokan aiki na da yawa da su ka fi ni iya tafiyar da mulki da jama'a, saboda haka ni a shirye na ke in yi biyayya ga duk wanda ya zama shugaba na—amma ba in nemi shugabancin ba. Ba kuma wai tawa'ari'u ne kawai ya jefa ni ga wannan hali ba, ganin yadda shugabancin ke da hatsari ne shi ya sa na ke nesa-nesa da shi. Gara mu haɗu a ɗakin taro ko a shafukan mujalla a ko'ina a duniya, a yi karon-battar ilimi, da in zo ina ta rigima da mutane ba gaira ba dalili, duk kuma a kan son rai da son duniya!

**Wane buri ka ke son ka cimmawa a rayuwar ka ta malanta?**

Daɗa inganta yaɗuwar ilimi a tsakanin al'ummar mu, iyayentar (watau *mentoring*) da matasa manazarta masu tasowa, nusar da jama'ar mu muhimmancin bincike da kuma yin amfani da sakamakon binciken

wajen inganta rayuwar al'umma.

Ka sha yin rubucc-rubucc tare da saka hannu kai-tsaye a harkokin adabin Hausa (fim, waƙa, littafi). Shin ka gamsu da cewa ka cimma ƙudirin ka na kawo gyara a waɗannan wuraren ko kuwa har yanzu jiya i yau ne?

Bari in gyara wata fahimta, wanda gyaran zai zama bambaraƙwai! Ba burin manazarci ba ne ya 'kawo gyara' a duk fannin da ya nutsa ya na bincike a kai. Ana nazari ne domin fahimtar yadda rayuwar jama'a ta ke, da kuma yadda ilimi ke samuwa ta wannan nazarin. A dai irin nazarin da mu ke yi, ba mu na yi ba ne wai domin a 'gyara', domin ba wanda ya san daidaito a harkar fasaha. Daidan wani karkataccen wani ne. Bari in ba da misali.

A yanzu haka ana taƙaddama a kan finafinan Hausa-Indiya, watau galibi na Indiya waɗanda ake fassarawa da Hausa. Idan ka je shafin *Freedom Radio* a *Facebook* za ka ga taƙaddama ta kaure tsakanin mabambanta ra'ayi har sau 1,852 daga ranar 15 ga Oktoba 2014 kawai.

Ina nan ina nazarin faruwar lamarin sosai – daga ɓangaren masu yi, zuwa ɓangaren waɗanda ba so so a yi. Magana ta gaskiya, ba ruwa na da duk ɓangarorin – ko su ci gaba ko a daina. Damuwa ta ita ce ana yi, kuma ina nazari, domin sanar da duniya ga wani sabon abu wanda bai taɓa faruwa ba a nazarin nishaɗin hululu a Afrikiyya, wanda kuma wani nau'i ne na *contra-flow*, watau wuta a masaƙa. Idan na gama aka buga maƙalar ko littafin da zan rubuta, shi kenan, sai in ci gaba da wani abin kuma – ba ruwa na da ko za a daina ko ba za a daina ba, domin ba 'gyara' na zo yi ba, nazari na zo yi. To haka lamarin ya ke ga sauran nau'o'in fasaha.

Harkar fim, wadda ta na cikin al'amuran da ka ke so su inganta, ta na cikin mawuyacin hali yanzu, musamman tun shigowar finafinan Indiya da ake fassarawa da Hausa. Wace shawara za ka ba 'yan fim domin su fita daga cikin matsalar da harkar su ke ciki yanzu?

Na ɗan taɓa wannan batun a amsar da na bayar ɗazu, amma bari in ɗan faɗaɗa, tare da ɗora bayanin bisa doron tarihi.

A lokacin da na shigo nazarin finafinan Hausa a shekarar 2000, ban shigo da wata niyyar samar da hanyar inganta sana'ar ba, domin ina bin sharuɗɗan nazari. Ba ni na fara yin binciken ba, Brian Larkin ne daga Barnard College, Columbia University, New York, ya fara. Da ya gama, bai bada waɗansu shawarwari na a yi gyara ba, domin ba ruwan manazarci da yin hakan.

Da na shigo sai ya zama ina da huluna biyu – ɗaya ta manazarcin da ba rowan sa da ko a yi gyara ko kada a yi; sannan ɗayar ta Musulmi, Bafillace, wanda ke da alhakin taimaka wa al'ummar sa ta kowacce hanya. Wannan hular ta biyu ba ni na ɗora wa kai na ba. Wanda ya ɗora min ita shi ne Ahmad Salihu Alkanawy, wanda shi ne jagora na na farkon shiga ta nazarin finafinan Hausa, wanda kuma na ke girmamawa sosai saboda ilimi da fasahar da Allah Ya yi masa. Da farko noƙewa na dinga yi, domin in zama matsayin 'ɗan ba ruwan mu' (*non-participant observer*), wanda wani ne daga cikin nau'o'in tattaro bayanai lokacin bincike. Amma da lallami da magiya Alkanawy da kuma sauran masu ra'ayi irin nasa na cewa sai an shigo da manazarta cikin sana'ar domin a yi mata gyara, aka cusa min wannan hular ta biyu; kai, har rijista ma na yi da ƙungiyar 'yan wasa a matsayin ɗan wasa, kuma ni a waje na har yanzu Shehu Hassan Kano shi ne shugaba na! Amma na ji an ce an rushe duk waccan rijistar!

Saboda haka da yawa mutane na ganin hular tawa ta biyu ce, domin na jingine hular ta farko. Ta wannan na shiga sana'ar domin neman 'gyara'. Na kafa majalisa ta farko a Intanet a 2001 domin bai wa 'yan wasan Hausa damar su sanar da duniya abin da su ke ciki. A lokacin ba na jin akwai mutane fiye da biyar 'yan wasan Hausa da su ka san Intanet ko kuma su ke da imel. Kada ma a yi maganar *Facebook*, domin ba a kirkiri *Facebook* a Amurka ba sai 2004, kuma ba ta zo nan ba sai wajen 2009 – ka ga mun girmi *Facebook* da shekaru da dama. A wani lokacin kuma ni ne na jagoranci wani kwamiti da aka kafa domin samar da gyara a cikin shekaru goma masu zuwa a sana'ar finafinan Hausa. To amma me zai faru, sai tsangwama, zagi, cin mutunci, da cewa ina yi musu hassada daga 'yan fim da mabiyan su.

Ga misalai. Wata tsohuwar 'yar wasa, wacce kuma har yanzu ta na fitowa a fim, ta shigo inda mu ke a Intanet ta zazzage mu, ta na cewa ban da gulmar 'yan fim ba abin da mu ke yi. Wani furodusa ɗan Kaduna ya zama ba shi da wani abokin gaba sai ni. Wani tsohon ɗan wasa ma har ɗura min ashar ya yi a wani taro a Kano, kuma ma a BUK, don na nuna cewa ba shi ne na farkon yin wata fasaha a fim ba. Wani sabon ɗan wasa ƙarara ya kira ni maƙaryaci a bainar duniya domin waya ya yi wa Freedom Rediyo a Kano, ya faɗi haka, wanda har sai da Gwaggo na ta kira ni ta ce kada in ƙara kulawa da 'yan wasan Hausa saboda abin ya yi mata zafi. Shi dai wannan ɗan wasan a baya sai da ya yi min gorin 'kowa ya raina tsayuwar wata ya hau ya gyara', kuma labari ya ishe ni cewa shi a duk duniya ba abin da ya fi yi masa daɗi kamar waɗannan kalaman wai don kawai su bai wa Farfesa haushi, saboda haka ko ba komai ya ci mutucin farfesa ɗin da wai ake ji da da shi. Waɗansu 'yan wasan, su ma a rediyo, cewa su ka yi ba ni da tunani. Wani tsohon ɗan wasa gori ya yi min wai sana'ar fim ta sa ina tafiye-tafiye. Na sanar da shi na fara tafiya ƙasar waje domin nazarin ilimi a 1981 zuwa ƙasar Ingila, kuma zuwa 2000 da na shigo fagen nazarin finafinai, na zauna a France, United States da Italy, ba kuma zaman ɗalibin makaranta ba; zaman ma'aikaci, domin a United States har *Social Security* na ke da shi. Saboda haka in gori ne, ni ne zan yi wa masana'antar domin ni na fito da ita aka san ta a duniya ta hanyar Intanet har ma manazarta kamar su Graham Furniss (England), Onookome Okome (Canada), Jonathan Haynes (United States), Carmen McCain (United States), Heike Behrend (Germany) da Mattias Krings (Germany) su ka san da ita su ke nazari a kan ta, kuma su ke ƙoƙarin samar mata murya a idon duniya. Kai, da dai sauran hayaniyar 'yan fim! Na sha su!

Saboda haka ba a taɓa samun manazarci da aka yi wa irin wannan cin mutuncin ba a bainar jama'a, sai ni, wai kawai don ana tunanin na ce a yi gyara. Ni kuma ba inda na ce ba a iya ba, ballantana in ce ga yadda za a yi. Ko a yi daidai, ko kada a yi, ba ruwa na. Aiki na in kalla, in naɗa, in rubuta, in sanar, in yi tafiya ta.

Kalubalen da na samu daga 'yan fim ya saɓa da yadda waɗansu daga cikin manazarta labaran hikaya na Hausa su ka fito ƙarara su ka soki littattafan da cewa shirme ake yi – amma da ya ke marubuta sun saba da muhawara, ba wanda ya fito ya ci zarafin waɗannan manazartan; hasali ma daga baya duk aka haɗe aka zama ɗaya domin ciyar da rubutu gaba. Amma ban da 'yan fim. Ko tari ka yi in ka na kallon fim ɗin waɗansu cewa za su yi hassada ka ke yi musu; shi ya sa ma na daina kallon kowannen fim ɗin Hausa sai dai in ina son in yi nazari a kan sa, kuma wannan ba wanda ya isa ya hana ni yin nazarin, kuma in faɗa wa duniya abin da na fahimta.

Tsangwamar ta sa na cire wannan hular ta biyu, na mayar da hula ta ta farko. Saboda haka a yanzu ba ni da wani burin in ga ko an gyara ko ba a gyara ba a sana'ar finafinan Hausa.

Kuma abin tambaya ma shi ne, ta na bu□atar wani gyara ne? Ga su nan birjik kullum ana sayarwa, masu yi su na harka, ana hawan manyan motoci ana gina katafaren gidaje, saboda haka wane gyara za kuma a bu□ata? Wanda ta ke yi da shi, ta na yi, wanda ba ta yi sai ya canza sana'a, ko da gada ya yi.

Amma kuma wannan ba ya na nufin ba zan taimaka ba wajen gina sana'ar, domin ai ba duk aka taru a ka zama □aya ba. Fiye da kashi 95 cikin ɗari na 'yan fim na □aruwa daga nazarin da mu ke yi, kuma su na son mu'amalar. Kai, za ma ka iya cewa □alilan da su ke hargowar, wa□anda kuma su ka fi kowa nasara a sana'ar, ba ma ahalin Hausawa ba ne, saboda haka dole su firgita in an yi nazari a kan finafinan da su ke yi. Amma kuma abin mamaki sun ƙi su yi fim a nasu yaren, sai da Hausa, wacce kuma, wani ƙarin abin mamakin, su ka tsana, domin gani su ke ta danne su.

Saboda haka mu na taimaka wa ragowar kashi 95 ɗin da ke neman taimakawa domin su inganta sana'ar su, kuma a nan zan iya cewa ina daga cikin masu tallafawa ainun. Misali, ni na jagoranci taron duk duniya a kan sana'ar fim a 2003, wanda aka wallafa littafin da ba a taɓa yin irin sa ba a lokacin, wanda kuma ana nazarin sa a jami'o'i da dama a Amurka.

Sannan da gwamanatin Kano ta shirya kafa makarantar koyon sana'ar

fim, ni aka naɗa in jagoranci kwamitin kafa makarantar. In da na biye ta zuciya ta, ba zan karɓa ba; amma saboda sanin cewa zan taimaka wa mutanen mu su yi fim wanda duniya za ta gani ta yarda da shi, ya sa na karɓa. Ni na ƙirƙiro da kusan kashi 95 cikin ɗari na manhajar da za a yi amfani da ita wajen koyarwar. Hatta kayan aikin da za a saya, ni na samo su aka saka su a rahoton mu. Ni na ba da tsarin koyarwar na rana-rana a makarantar, watau *Time-Table*. Ni na ba da sunayen malaman da za su koyar.

Da Gwanatin Tarayya ta bayar da tallafin wani horon 'yan fim a tsarin *Project ACT Nollywood*, ni na kawo shawarar a ƙirƙiri *Filaps Media Training Institute* domin a yi aikin. Ni na tsara karatun, na kuma jagoranci aiwatar da koyarwar har tsawon sati shida.

Ko a BUK – inda na ke koyar da Dabarun Fim (*Filmmaking Techniques*) daga cikin kwasa-kwasan ilimin sadarwa—ina daga cikin malaman da ke kiran 'yan fim su zo su yi wa ɗaliban mu lacca. Ta haka na gayyaci Mika'il Gidigo ya zo ya yi wa ɗalibai *Film Master Class* inda ya nuna musu dabarun ɗaukar fim. Abdulkareem Mohammed ma ya zo ya yi koyarwa har ta wata uku. Sannan nan gaba, insha Allah, za a gina mana *Faculty of Communication and New Media Studies*, inda za a ware mana soron tsangya sukutum mai suna *Department of Visual Communication* inda za a koyar da *B.Sc. (Hons) Cinematography*. Niyya ta ita ce mu jawo 'yan fim da dama a matsayin Matallafan Mallamai, watau *Adjunct Lecturers*, domin yin amfani da basirar su da sanin su wajen tallafawa a lokacin koyar da waɗansu kwasa-kwasan. Ina yi wa sana'ar hassada zan yi waɗannan abubuwan?

Saboda haka alhamdu lillah, Allah Ya ara mana damar da za a yi abubuwan da za su taimaka domin ci-gaban mutanen mu. Zagi, tsangwama da cin fuska kuma ba za ka hana mutane yi ba—sai su ci gaba, da fatan Allah Ya shirye su.

**Ta fuskar nazari, ko akwai haɗarin da ka hango wa al'adun Hausa da shigowar finafinan Indiya da ake fassarawa da Hausa?**

Babu. In da akwai, to da tuni jama'a su sun gurɓace saboda kallon ainihin finafinan Indiyan, ba na fassarar ba. Ba yadda waɗannan finafinan Indiyan—kai ko ma na wacce ƙasa—za su samu tasiri a kan al'adun Hausawa; shi ya sa ma ba mu cika mayar da hankali a kan wai tasirin baƙin al'adu a kan al'ummar Hausawa ba ta hanyar hanyoyin sadarwa. Ai mun jima mu na kallon finafinan Amurka, amma ba wata gurɓata da za a auna a ce wai kallon finafinan ne ya kawo haka, duk da ƙazantar su, wacce ta fi ta Indiya.

Sannan kar ka manta, tun daga watan Nuwamba 1960 aka fara nuna finanfinan Indiya a *Palace Cinema* da ke Kano, ya zuwa yanzu. Fim ɗin farko na Indiya da aka fara nunawa a silima a Kano shi ne *Changez Khan*, wanda Kedar Kapoor ya yi darakta a 1957. An nuna finafinan sun fi dubun dubata—kuma jama'ar mu na ta kallon su; tun ba sa gane yaren, har su ka iya; yanzu ma akwai masu alfaharin waƙa da kuma magana da juna a cikin yaren Indiyanci (amma na fim, don yararrakin Indiya su na da yawa). Wannan ya gurɓata mutanen mu? Ka ga ana tallar abincin Indiyawa kamar *Baigan bharta*, *Dum Aloo*, *Chapati* ko *Tandoori Chicken* a kasuwannin mu? Ko mace ta sa *Sari* ta fito? Ko namiji ya ɗaura *Dhoti* (wanda zani ne; duk ko wanda ya yi haka za a ce ɗan daudu ne!). Ko ka ga mutum ya saka wa sunan ɗan sa wani sunan Indiya—ko su kan su masu mayatar Indiyancin a finafinan su ba sa haka. Waɗannan kuma su ne al'adu.

Damuwar shi ake kira da *Media Effects Theory*, ko kuma *Cultural Imperialism*. To amma Musulunci ya kafu a zuciyar mutanen mu ta yadda ba yadda wani ashararanci—komai birgewar za da dai yi—zai zo ya canza al'adun mu. Su kan su Hukumar Tace Finafinai ba su nuna damuwa da haka ba saboda sun san ba yadda za ka danganta taɓarɓarewar al'ada da kuma kallon fim. In mutum ya lalace, da ma can lalatacce ne tun daga gida, kira kawai ya ke jira.

Masu surutun gurɓatar al'adu a wannan fassarar 'yan fim ne, ko waɗanda kasuwar su za ta taɓu, amma ba mutanen gari ba, domin ɗan zantawar da na yi a fagen binciken wannan al'amarin ya nuna jama'a da dama sun ma daina kallon finafinan Hausa, sun fi son waɗannan Hausa-Indiyan ɗin. Kamar yadda na ce, ka shiga shafin Rediyo Freedom a *Facebook* kaga muhawa fiye da 1,850 a kan wannan batun—kusan da yawa goyon bayan fassarar su ke yi. Su ma waɗannan duk hassada su ke yi wa 'yan fim kenan? Saboda haka nan ne 'yan fim ya kamata su mayar da hankali, ba wai manazartan jami'a ba.

Sannan kuma damuwar 'yan fim da Hausa-Indiya na ba ni mamaki. Su ne fa su ke alfahari da satar basirar kwafo finafinan Indiya su juya su, su zama na Hausa – ba wanda ya ce da su uffan. Kusan duk fim ɗin Hausa da ka gani yanzu ya na da tushe a wani fim na Indiya, kuma har alfahari ake da yin haka—daga sababbin har tsofaffin 'yan fim ɗin. Sai wani ya kawo tunanin a yi fassara kai-tsaye zuwa Hausa daga lafazin Indiya, maimakon a ɓata kuɗi da lokaci a wanke fim ɗin. Don me 'yan fim za su damu? Ba fim ɗin ka aka taɓa ba – wanda shi ma asali ba fim ɗin ka ba ne, satowa ka yi da ga Indiya. Idan 'yan fim sun ce ana kashe masu kasuwa, ba su ne su ke iƙirarin sun kashe kasuwar finafinan Indiya a ƙasar Hausa ba – ko don su Indiyawan ba su da bakin ƙorafin an kashe masu kasuwa? Kuma nawa su ke biyan su ladar sato finafinan su, su na juya su zuwa Hausa? Ashe sata ce ta saci sata!

Idan su na gudun wai akwai tarin jama'a da yawa masu ci daga yin fim, to ai kamar yadda Babban Darakan Hukumar Tace Finafinai ya ce a hira da Nasiru Zango a Freedom Rediyo, 'yan fim kamata ya yi su inganta sana'ar su ta yadda za su jawo masu saya. Mun ba su shawarwari, sun ce 'kowa ya raina tsayuwar wata, ya hau ya gyara', ga shi kuma har yanzu watan nasu a karkace ya ke! Duk masu ci da sana'ar fim za su iya ci gaba da yin haka idan sun yi fim ɗin da jama'a za su saya, maimakon ƙorafin sana'ar wani. Kada kuma ka manta, daga cikin 'yan fim ne fa aka samu masu sana'ar fassarar!

Saboda haka mu a nazarce ba ruwan mu – ko za a fassara na Indiya, ko Cana, ko Rasha zuwa Hausa bai shafe mu ba, domin ai mutanen mu na ganin na Turanci, kuma su na gane abubuwan da ke faruwa – wanda ƙazantar su ta fi ta Indiya – amma wannan bai sa al'adun su sun gurɓace ba duk da yawan finafinan Amerikan da mu ke saya.

**Da yawa ana kallo ka a matsayin sarkin aiki. Ko yaya Malam ya ke ya na hutawa?**

Wallahi ina hutawa sosai. Akasari na kan je majalisar mu a Daneji da yamma, bayan na gaida iyaye na, mu zauna a yi ta hira. Sannan a gida na kan narki barci duk lokacin da ya kama ni! Na dai fi yin aiki daga ƙarfe 8.00 na dare zuwa ƙarfe 3.00 na safe, watau kusan asuba kenan, domin garin lokacin tsit ya ke! Kawai dai ba ni da wani abin da ya wuce nazari da bincike. Ko kallon bal ba na yi, domin ban iya ba, kuma wannan zurawar a guje da ake yi har juya min kai ya ke yi domin ba zan iya ba!

**A ƙarshe, ina za ka fuskanta a fagen nazari? Domin akwai alamun ba ka iya tsayawa a wuri ɗaya!**

Ka san zama wuri ɗaya hatsari ne, in ji kifi! Tabbas kam na fara karkata akala ta zuwa wani sabon fagen.

Na jima in sha'awar zurfafa bincike a kan Larabawan Hausawa, watau jama'ar da ke da alaƙa ta halitta da Larabawan da su ka fito daga Tunisia, Morocco, Libya, Egypt, Jordan, Lebanon, Yemen da kuma Sudan. Kakannin waɗannan sun shigo ƙasar Hausa da jimawa, kuma sun saje, sun auri matan Afrikiyya, watau baƙaƙe. Shin waɗanda su ka haifa, watau waɗanda mu ke gani yanzu, yaya su ke ganin kan su – Larabawa ko Hausawa? Mahaifi na, Dr. Muhammadu Uba Adamu, shi ya fara wannan nazarin a kan gudunmawar Larabawa ga al'ummar Kanawa, inda ya buga maƙalar sa a kan wannan a 1968.

Muhimmancin wannan shi ne tabbatar da cewa wanene Bahaushe? Domin a yanzu manazarta sun rabu gida biyu. Akwai waɗanda ke ganin cewa Hausa yare ne – duk wanda ya iya, ya zama Bahaushe. Akwai kuma waɗanda ke ganin cewa Hausa ƙabila ce, in ba ka ahalin ƙabilar to kai ba Bahaushe ne ba, ahalin kuma su ne garuruwan Daura, Katsina, Gobir (wanda ya haɗa har da Maraɗi, Zinder da Niamey), Kano, Rano, Zazzau da Biram (Haɗeja). Waɗanda za mu samu su nuna mana gaskiyar lamarin su ne Larabawan Hausawa. Ga su dai Larabawa ne a fata, amma kuma ba su iya Larabci ba, sai Hausa. Shin a wane rukuni za mu saka su? Larabawa (saboda fata da asali) ko kuwa Hausawa (saboda ban da Hausa ba wani yaren da su ka sani)? To ka ji inda zan kutsa kuma!